Lalle mumini yana riska da kyawawan dabi’unsa matsayin mai azumi da mai tsayuwar dare

Daga Aisha - Allah Ya yarda da ita - ta ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - yana cewa: Lalle mumini yana riska da kyawawan dabi’unsa matsayin mai azumi da mai tsayuwar dare.
[Ingantacce ne a baki dayan ruwayoyin sa] [Abu Dawud ne ya Rawaito shi da Kuma Ahmad]

Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana bayyana kyawawan ɗabi’u suna kai mai yin su matsayin mai azumi kullun da rana kuma mai Nafila da daddare, matattarar kyawawan ɗabi’u ita ce: bayar da kyakkyawan abu, da kyakkyawar magana, da sakin fuska da rashin cutar da mutane da jure cutarwarsu.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/5799